


Gandun Manyan Dabbobi
Littafin karatu a sauƙaƙe - Mataki na 3
Hausa

Zuwa ga malamai da iyaye:

Kafin a fara amfani da wannan tsarin koyon karatu, dole sai ɗalibi ya: • San amon sautukan haruffan Hausa; • Iya gane kalmomin da aka saba da su.

Gandun Manyan Dabbobi
Hausa Nigeria

Copyright © 2017, Enabling Writers Project -American University of Nigeria

http://creativecommons.org/licenses/by/4.0/

http://creativecommons.org/licenses/by/4.0/ An yarda ka yi amfani da wannan aikin ta wajen harkar kasuwanci. Kana iya ɗaukar aikin nan a yadda ya ke ko ka yi ƙari akai. Dole ne ka ajiye haƙƙin mallaka da kuma alaƙanta aiki ga marubuta, masu zayyana da sauran su. ISBN


Grace Malgwi Writing Trainer/Collection Editor

Prof Salisu Yakasai and Prof Lawan D Yalwa Hausa Language Consultants


Nas Yakubu Bloom Trainer


Story Writers Husaini Adamu; Adamu Babbikoi; Garba Mohammed Dantsoho; Jalauddeen Ibrahim Maradun; Yasalu Haruna; Muhammed Umar Deba; Idris Hamid; Ibrahim Baraya; Dahiru A Yelwa; Mansur Isah Buhari; Grace Malgwi


Illustration from International Illustration:The Art of Reading 3.0 Copyright: SIL International 2009




An yi wani zaki sarkin dawa.
Zaki ya kore ƙananan dabbobi daga dawa.
Ya ce ba ya sarautar ƙananan dabbobi.














Sarki ya kori kunkuru da zomo.
Ya kori tsuntsu da biri.
Ya kuma kori zakara da ɓera.















A cikin dawan sarki sai manyan dabbobi.
A dawa akwai giwa da doki.
Akwai koma jakin-dawa da damisa




Wata rana zaki ya faɗa cikin raga.
Dabbobin dawa sun ji kukan zaki.
Dukansu sun fito su taya sarki.













Giwa ta ja raga da hanci.
Doki ya taka raga da ƙafafonsa.
Zaki bai samu tsira ba.












Dukan manyan dabbobin dawa sun kasa.
Jakin-dawa ya ce a nemi ɓera.








Sarki ya ce ɓera ba ya dawansa.
Jakin-dawa ya ce sai a nemo ɓera.



Jakin-dawa ya sami ɓera.
Ɓera ya tsinka raga da haƙoransa.
Zaki ya sami tsira.



Kananan dabbobi sun dawo cikin dawan zaki.
Manya da ƙananan dabbobi sun zauna lafiya.
Kowace dabba na da muhimanci.

ALL CHILDREN READING: A GRAND CHALLENGE FOR DEVELOPMENT

USAID FROM THE AMERICAN PEOPLE

World Vision

Australian Aid

GLOBAL READING NETWORK